Abincin Yini



Fahariya da Gicciye

Yesu ya ɗauki kunyarmu domin mu sami ɗaukakarsa



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Wata rana, Ruhu Mai Tsarki ya yi mani magana ta wurin harsuna da fassara: "Ka dubi aikin Kalfari, cikakken aiki; cikakke ta kowane fanni, cikakke a cikin kowane abu." Allah ya nuna mani cewa idan zan iya fahimtar cikakken abin da Yesu ya yi a kan gicciye a Kalfari, zan gane cewa cikakke ne, kammalalle ne. Babu wani abin da ake buƙatar ƙarawa, babu abin da za a iya ragewa daga cikin shi. An biya kowace buƙata. Wannan ya sa ina so in ƙara sani game da gicciye. A hankali, a wasu shekaru, Ruhu Mai Tsarki ya bani ayoyi masu yawa.

> "Amma ni daɗai ba ni yin fahariya, sai dai cikin gicciyen Ubangijinmu Yesu Kristi, wanda an gicciye mani duniya ta wurinsa, ni kuma an gicciye ni ga duniya." (Galatiyawa 6:14)

Bulus yana da abin fahariya guda ɗaya kawai - gicciyen Ubangijinmu Yesu Kristi. Wannan magana ce mai ban mamaki idan aka yi la'akari da cewa a zamanin Bulus, gicciye shi ne cikakken misali na dukan abin da kunya da ban ƙyama suka ƙunsa.

A cikin littafinsa Likita a Kalfari, Pierre Barbet, wani likitan fiɗa na Katolika, ya yi ƙoƙarin ganowa da kuma bayyana ɗanɗano zafin jiki na mutumin da aka gicciye. Matsalar ita ce babu wani abin gwajin da za a iya gwadawa da shi domin babu wanda a da can a ƙarnoni biyu da ya taba ganin wanda aka gicciye. Wannnan ya zo mani cikin tunanina yadda gicciyen ya yi nisa a gare mu a matsayin kayan aikin kunya da azabtarwa.

Bulus bai yi alfahari da asalin sa na Bayahude ko Ikkilisiyun da ya kafa ko kuma mu'ujizan da ya gani ba. Ya yi alfahari da gicciye ne kawai. Bari wannan ruhun ya kasance a cikin kowannen mu - ruhun da ba zai yarda da fahariyar jiki, girman kai, da wadatar kai ba - domin mu iya amincewa da gicciyen Yesu Kristi cikin tawali'u.

Na gode maka, Yesu, saboda aikinka a kan gicciye. Ina furta cewa zan yi fahariya da gicciyen Yesu Kristi, domin Yesu ya ɗauki kunyata domin in sami ɗaukakar Sa. Amin.

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-139-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 24 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources



© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.